Badaɗayina - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi mini wasicci da (abubuwa) uku: Azimin kwana uku a kowane wata, da raka'o'i biyu na walaha, kuma in yi witiri kafin na yi bacci

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Badaɗayina - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi mini wasicci da (abubuwa) uku: Azimin kwana uku a kowane wata, da raka'o'i biyu na walaha, kuma in yi witiri kafin na yi bacci.
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - yana bada labarin cewa masoyinsa kuma abokinsa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi masa wasicci kuma ya alkawaranta masa ɗabi'u uku: Na farko: Azimin kwana uku a kowane wata. Na biyu: Raka'a biyu ta walaha a kowace rana. Na uku: Witiri kafin bacci; hakan ga wanda ya ji tsoron kada ya farka a ƙarshen dare.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/4538